East African Scholars Journal of Education, Humanities and Literature

*Abbreviated Key Title: East African Scholars J Edu Humanit Lit*
ISSN: 2617-443X (Print) & ISSN: 2617-7250 (Online)
Published By East African Scholars Publisher, Kenya

OPEN ACCESS

Volume-4 | Issue-1 | January- 2021 | DOI: 10.36349/easjehl.2021.v04i01.005

**Review Article**

# Bori Da Girka A Bahaushen Tunani: Duba Cikin Waƙar Bahaushen Girka Ta Sulaiman A. Tijjani

Yunusa Ibrahim Adamu*

Center for Hausa Studies, Usmanu Danfodiyo University, Sokoto

**Article History**
Received: 13.01.2021
Accepted: 25.01.2021
Published: 30.01.2021

**Journal homepage:**
https://www.easpublisher.com

**Quick Response Code**

**Tsakure:** Sau da dama akan samu dangantaka tsakanin al'ada da adabin Bahaushe. Irin wannan dangantaka ce za a tarar yayin da aka nazarci waƙar *Bahaushen Girka* ta Sulaiman A. Tijjani. Dalili kuwa shi ne, a cikin waƙar ya zayyano al'amuran da suka shafi al'adar girka daki-daki. Wannan takardar ta mayar da hankali wajen nazarin waƙar domin fito da muhimman kalmomi da Sulaiman Tijjani ya yi amfani da su da ke da alaƙa da al'adar bori da girka. An bi manyan hanyoyi guda biyu domin gudanar da wannan bincike. Hanya ta farko ta shafi nazarce-nazarcen ayyukan da suka gabata masu dangantaka da binciken. Bayan haka kuma, an yi ziyarar gani-da-ido zuwa wuraren da ake gudanar da bori domin samun ingantattun bayanai daga tushe. Sakamakon binciken na nuna cewa, mawaƙin ya yi ƙoƙari wajen samar da bayanai masu inganci game da al'adar girka. Dangane da hakan ne takardar ke ba da shawarar cewa, a ba da ƙaimi wajen nazartar ire-iren waɗannan waƙoƙi da ke ƙunshe da al'adun Hausawa.

**Muhimman Kalmomi:** Bori; Girka; Bahaushen Girka; Waƙa; Al'ada.

**Copyright © 2021 The Author(s):** This is an open-access article distributed under the terms of the Creative Commons Attribution **4.0 International License (CC BY-NC 4.0)** which permits unrestricted use, distribution, and reproduction in any medium for non-commercial use provided the original author and source are credited.

## GABATARWA

Adabi wani lamari ne mai matuƙar muhimmanci a wajen kowacce al'aumma. Sai dai manazarta Adabi suna amfani da kalmomi biyu wajen bayyana rayuwar Bahaushe ta asali. Kalmar 'adabi' ta fi shahara a bakin manazarta ko masu ilimi [1]. Ita kuwa Kalmar 'al'ada ta fi zama a bakin mutanen gari da kuma masana addini [2]. Amma duk da cewa manazarta suna kallon Kalmar a matsayin 'adabi', a iya cewa idan ka ambaci adabi dole sai ka fassara wa mutanen gari abin da ake nufi da kalmar. Domin an yi ittifaƙin cewa adabi yana da rassa biyu, wato na baka da rubutacce [3].

Ita kuwa Kalmar 'al'ada' ita ma ararriya ce daga harshen Larabci, wacce ita a gangariyar Hausa ake cewa 'gargajiya'. Sai dai yarda da addinin musulunci ne ya sa, Bahaushe ya maye gurbin kalmar gargajiya da ta al'ada. Sakamakon yadda duk wani lamari da Bahaushe yake son ya kauce masa sabo da tasirin addinin musulunci. Hakan ya sa da wuya ka ji an ambaci kalmar gargajiya, sai dai a ce al'ada. Dan haka al'ada ita ce hanyar rayuwar kowacce al'umma. Ita ce hanya ɗaya tilo ta rayuwar kowanne mutum tun daga haihuwarsa da balagarsa da girmansa da Aurensa da kuma mutuwarsa [4].

### Manufar Bincike

Manufar wannan bincike shi ne wayar da kan Manazarta game da lamarin Bori da kuma Girka. A irin wannan manufa ne, za a ga yadda za a samar da wani bayani mai ɗauke da yadda tsarin Bori yake faraway. Kafin mutum ya zama cikakken Ɗan Bori, har wani yanayi ya sa a yi masa girka. Wata Manufar kuma ita ce samar da abin karantawa ga Ɗalibai da masu sha'awar Nazarin harshen Hausa. Da nufin inganta ɓangaren Adabin Bahaushe da kuma Al'adunsa. Haka kuma yana daga cikin Manufar wannan bicike yin hannunka mai sanda domin a san yadda lamuran suke, sannan a rairaye tsakuwa daga cikin tsakin. Wato a ɗauki masu amfani da adana Tarihi, kuma a watsar da Baragurbin.

### Dabarun Bincike

Bahaushe ya yi gaskiya da ya ce "Kowanne bakin wuta, da nasa hayaƙi" Kamar kowanne bincike ita ma wannan takarda ta yi amfani da irin nata dabarun domin ganin kwalliya ta biya kuɗin Sabulu. Da farko dai an kunna nutso a cikin waƙar 'Bahaushen Girka' wacce Sulaiman Ahmad Tijjani ya rera. Sai da aka tabbatar an fitar da tsoka daga ƙashi kafin ma fara wannan aikin. Sai kuma duba manya da ƙananan kundayen bincike masu alaƙa ta kusa da wannan aikin. An sake duba manyan litattafan adabi da al'ada dan wannan bincike ya samu nasara. Sannan an je ƙafa ya

ƙafa wajen da ake aiwatar da lamuran bori da girka, dan zama ganau ba jiyau ba. A ƙarshe kuma an tattauna da ƙwararru a harkar bori da girka da bayar da magungunan gargajiya, duk dan wannan aikin ya yi nasara.

**Taƙaitaccen Tarihin Sulaiman Ahmad Tijjani (Farfesan Waƙa)**

A wata hira da Sulaiman Ahmad Tijjani ya yi a cikin shirin 'Hikima Taguwa' na gidan Rediyon Garkuwa Fm. Dake birnin Sakkwato. Ya bayyana cewa an haife shi a ƙauyen Paki dake yankin ƙaramar hukumar Ikara ta jihar Kaduna. A ranar 2 ga watan Fabaraiyun, 1985. Yanzu haka yana da shekaru 36. Ya yi karatun Firamare a makarantar Paki Central Primary School, ya kuma yi ƙarama da babbar Sakandare a Sakandaren Paki da ake kira da GSS, Paki. A inda ya kamala a shekarar 2010. Ya ce " A gidanmu muna da wata al'ada ta idan Yaro ya kammala karatun Firamare, akan zaunar da shi a gida da nufin koyar da shi ilimin addinin Islama. Tun daga kan karatun Allo na Alƙur'ani mai tsarki, da kuma litattafan koyon tsarki da koyon Tsarki da Alwala da kuma Sallah". Bayan ya gama irin waɗancan litattafai, sai ya wuce GSS, Paki kamar yadda aka faɗa a baya.

Sulaiman, ya fara waƙa ne tun yana Yaro ƙarami, mutum ne mai son yawan yin rubutu na zube da 'yan waƙoƙi. Sai dai abin da zai iya tunawa shi ne, a shekarar 2011 ne ya tsunduma a harkar waƙa sosai da sosai. A lokacin ne ya fara zuwa Sitidiyo domin buga waƙa. Wannan a taƙaice Kenan.

Bayan an ji ta bakin masana game da adabi da kuma al'ada, abu na gaba a cikin wannan maƙala za a duba yadda Bahaushe yake kallon Bori da Girka, da yadda aka yi baje-kolin al'adu a cikin Waƙar 'Bahaushen girka' wacce Mawaƙi Sulaiman A. Tijjani da aka fi sani da Farfesan waƙa ya wallafa.

**Bori**

Wata hanya ce ta bautar Iskoki, kamar yadda Musulmai ke bautar Allah (SWT) da nufin neman biyan buƙata [2]. Haka kuma Bori wata daɗaɗɗiyar al'ada ce da ake yi a ƙasar Hausa tun kafin zuwan addinin Musulunci. Hanya ce da ake bi wajen bautar iskoki a matsayin addini. Domin nema da samun dukkan buƙatu daga Aljanu ko Iskoki. Masu riƙo da wannan al'ada ta Bori, sun yarda kuma sun amince cewa bautar irin waɗannan Iskoki ita ce hanyar samun duk wani magani ga marasa lafiya ko masu lalura [5].

Sai dai sharuɗan dake cikin wannan addini na Bori shi ne, dole ne sai ka kasance kana da Iskoki da suke a kan ka ko kan ki, kafin ka zamo ƊanBori. Idan kuma kana da sha'awar ka shiga wannan addini kuma baka da irin waɗancan Iskoki, sai ka zauna da manyan Sarakunan Bori da manyan Bokaye a girka ka, kafin ka samu shiga cikin irin wannan addini.

Haka kuma Bunza [2], Ya raba Bori ya zuwa kashi huɗu kamar haka:

1. Borin Fage
2. Borin magani
3. Borin giri
4. Borin girka

A nan, wanna maƙala za ta fi mayar da hankali ne ga 'Borin girka' wanda a kan sa ne Sulaiman Ahmad Tijjani da aka fi sani da Farfesan waƙa ya gina waƙarsa ta 'Bahaushen girka'

**Girka**

Wannan na nufin kafe wani abu ko ɗora wani abu a kan wani da nufin a zaunar da wannan abin a kan wani. Za a iya tabbatar da wannan ma'ana idan aka dubi Kalmar 'Girki'. Kowa ya san cewa idan aka ce "Furera tana yin girki". Abin da mutum zai sa ran ya gani shi ne, ya ga an ɗora tukunya a kan murhu ana dafa abinci. Waccan ɗora tukunyar da ake yi a kan murhu, ita ce girkawar. Amma a harshen Bori idan aka ce 'girka' ana nufin zaunar da wasu gungun Aljanu ko Iskoki a kan wani Bil'adama da nufin su saba da shi su riƙa yi masa hidima, ta fuskar bayar da magungunan dukkan cututtuka. Sannan girka na daga cikin lamura masu wahalar aiwatarwa a cikin aikin Bori, domin sai an tanadi kayayyakin da za a yi amfani da su a wannan aiki na girka. Hakan ta sa ba a iya yin girka a lokaci guda. Kuma dole sai an yi tarayya da juna, wato mutum guda ba zai iya aiwatar da girka shi kaɗai ba.

**Bahaushen Girka**

Waƙar Bahaushen girka, waƙa ce da a cikinta mawaƙin ya zayyano ma'anar Bori da kuma Ɗan Bori. Da irin zurga-zurgar da ake yi kafin a zama ƊanBori. Har ya kwatanta shi da 'Hurtumin Sa' wato irin artabun da ake yi da gawurtattun Shanu. Da irin yadda suke dalalar da yawu mai yauƙi da kumfa kamar dai yadda Sa mai asurka yake yi. A gaba kuma ya ambace shi da irin Amalen Raƙuma, da irin tsallen da Amalen Raƙuma yake yi a dokar daji, ko a duk lokacin da wani abu ya taso, haka ƊanBori yake yi, a lokacin da ake yi masa girka.

An rera wannan waƙa ne domin zayyano lamarin Bori da kuma yadda idan lamura sun gawurta ake tashi daga ƊanBori gama-gari a koma 'girkakken ƊanBori. Kamar yadda mawaƙin ya faɗa tun a farkon buɗe waƙar kamar haka:

Jagora: Yin baitukan Bahaushen girka, na san muna da turka-turka

Farfesan Waƙa nai waƙa na bankaɗo Bahaushen girka

Har na aza shi bisa misalign nan na hurtumi na Sa da asurka

Amshi: Bauri da Bori ware bare baubauniya rawarsu ta dauri

Na bankaɗo Bahaushen girka

Amshi: Bauri da Bori ware bare baubauniya rawarsu ta dauri

Ya bankaɗo Bahaushen girka

Jagora: Yin baitukan Bahaushen girka na san muna da turka-turka

Farfesan waƙa nai waƙa na bankaɗo Bahaushen girka

Har na aza shi bisa misalin nan na hurtumi na Sa da asurka.

Tun a amshin waƙar Mawaƙin ya bayyana ma'anar Bori da cewa wani lamari ne da ya kangare ko kuma wani ya tashi daga asalin siffar da aka san shi. Wato ya koma wata siffar. Kamar a ce ka tauna Gyaɗa Bori, kana tsammani da ka tauna za ka ji garɗi a baki, amma sai ka ji ta sauya daga garɗin ta koma wani yanayi na da ban. Sai kuma ya ambaci 'Baubauniya' wato wata rawa da masu Bori ke yi, kafin ajanun su iso garesu. Sai kuma a ɗango na gaba ya shiga cikin waƙar da bayyanar da al'adun dake cikin addinin Bori da kuma yadda ake yin aikin girka, kamar haka:

Jagora: Ɗirkaniyar kiran 'yan kogo wane mutum ya rushe girka,

In an yi katarin haɗa komai sai ran shigar su wa Dokin ka,

Mai Kacakaura ga su garaya sautin a gane taken iska,

Gaɗa Ira'izai an ca-cum ga Julkukuwa mutanen girka,

Amshi: Bauri da Bori ware bare baubauniya rawarsu ta dauri

Ya bankaɗo Bahaushen girka

A ɗangon da ke sama Sulaiman A. Tijjani ya yi baje-kolin al'adun Bahaushe ta fuskar Bori da yadda ake yin girka. A inda yake gani wani babban al'amari ne, da Hausawa ke yi tun iyaye da Kakanni, wanda yake ganin zai yi wuya rana ɗaya a tsawatar, ko a hana aiwatar da Bori ko lamarin girka.

A bisa al'ada Garaya da Goge aka fi sani da kayan kiɗan 'Yanbori. Kayan kiɗa ne da kowa ya san ake amfani da su wajen kaɗa taken iskokin da ake son su zo dan su hau kan mutum. Ita garaya, abin kiɗa ne da ake yi da karamin Ƙoƙo da sanda da izga ko tsirkiya ake kaɗawa da 'ya'yan wuri. Ana samar da dukkan sautin da ake bukakata. Sai kuma 'Caki' shi kuma butar duma ce ake fafewa, idan ya bushe sai a rarake cikinsa akan zuba 'ya'yan tafasa ko na Zogale busassu. Sai a toshe bakin ta yadda 'ya'yan ba za su zubo ba. Da shi ake girgizawa, ana bugawa a ɗaya hannun da aka sa 'ya'yan wuri a jiki duk dan ya bayar da sautin da ake buƙata.

Bayan waɗannan bayanai da suka gabata, a yanzu wannan muƙala za ta kunna nutso a cikin wannan waƙa ta Bahaushen girka, domin yin taza da tsifa, wajen ganin an zaƙulo al'adun Bahaushe a ciki.

5. Jagora: Yin baitukan Bahaushen girka na san muna da turka-turka
   
   Amshi: Bauri da Bori ware bare

6. Jagora: Domin aza shi nan ga misali na Hurtumi na Sa da asurka,
   
   Amshi: Ya bankaɗo Bahaushen girka,

7. Jagora: Ranar shiga da rana ta fita bishiyar Kuka a nan zai wanka,
   
   Amshi: Baubauniya rawarsu ta dauri

8. Jagora: Mutantani su hau bisa Dokinsu sai mu ce Bahaushen girka.

Tun a ɗango na biyar da na shida da bakwai da kuma na takwas, Mawaƙin ya fara zayyano yadda ake girka kafin a zama cikakken Ɗanbori. Wato irin faɗi-tashin da ake yi kafin a kai ga nasara. Kamar yadda ya ambaci girka da kalmar turka-turka. Wato akan sha wahala sosai kafin a kai ga girka mutum ya zama ɗanBori.

Sai a ɗango na bakwai ya yi bayanin inda ake yin girka. Wato ƙarƙashin bishiyar Kuka, wanda bisa al'ada ba dole sai kuka ba, akwai bishiyoyi da yawa a ƙasar Hausa, da Bahaushe ya yi imanin cewa ana samun iskoki ko mutanen ɓoye a jikinsu. Irin waɗannan bishiyoyi sun haɗa da Tsamiya da Kuka da Tumfafiya da Marke da Zuwo da Kargo da Sabara da Danya da sauransu. Sai kuma ya ambaci ranar shiga da kuma ranar fita. A Bahaushiyar al'ada, akan shirya ranar da za a girka Ɗanbori ne, wato akan sanya wata rana da ake ganin cewa ita ce wacce ta fi dacewa da a kira waɗannan iskoki. Domin sun yarda cewa, idan aka sa wata ranar da ba ta zuwan iskoki ba, lallai in za akwana ana kaɗa garaya ko goge, ba za su zo ba. Dan haka a wasu lokutan akan sa ranar Lahadi ko Talata ne, su kasance ranar shiga. Wato ranar da za a fara wannan aiki na girka. Ya danganta da yadda aka tattauna da sarakunan Bori, ko manyan Bokaye. Domin sa irin wannan rana. Sannan wajibi ne a aike da goron gayyata ga mutane masu irin wannan sana'a ta Bori na kusa da na nesa, da nufin su hallara a wannan waje. Domin an ce "Kowanne bakin wuta da nasa hayaƙi". Wato kowa da irin gudun muwar da zai bayar wajen ganin wannan aiki na girka ya kai ga nasara. A lokuta akan sa kwana Bakwai ne ko fiye da haka. Ya danganta da yadda iskokin suka bayar da haɗin kai, wajen zuwan su da wuri.

A ɗango na takwas kuma sai mawaƙin ya yi magana a kan yadda iskokin suke zuwa su hau kan mutum, a inda ya ambace su da 'mutantani'. A al'adar Bahaushe, da zarar an fara kaɗa taken iska, duk inda ta ke, za ta zo ta hau kan wanda ake nufin girkawa ne. Wani lokacin sai an yi da gaske, sannan wata iskar za ta zo. Sukan ce ƙila an ɓata musu rai ne ya sa suka ƙi zuwa. Ko kuma ba a gama yin yarjejeniya da su ba ne. Wasu kuma salin-alin sukan zo su hau kan wanda ake so su hau.

9. Jagora: Ga tsagwaron tsumi tsumin tsanbauri, kayan shirin Bahaushen Girka,
   Amshi: Bauri da Bori ware bare

10. Jagora: 'Ya'yan wuri a nemo warki ranar bikin ga ba a kuka,
    Amshi: Ya bankaɗo Bahaushen girka,

11. Jagora: A Hausa nan ake al'ada girka kama ɗaukar jinka,
    Amshi: Baubauniya rawarsu ta dauri,

12. Jagora: Zobba da hannuwa da ƙafafu domin a samu yardarm iska.

A ɗangwaye na tara da goma da shaɗaya da kuma shabiyu, Malam Sulaiman Farfesan waƙa, ya yi ƙoƙarin fayyace wasu muhimman al'adun da ake yi a lokacin yin girka. Da farko ya yi Magana a kan wani tsumi da ake amfani da shi. Dole ne kafin a girka mutum ya zama Ɗanbori, sai an yi masa wani tsumi, a inda ake samun sabuwar 'kwatarniya' a cika ta da ruwa, sai a bazama cikin daji a sassako wasu itatuwa da saiwoyi da ganyayyaki, wasu lokutan ma har da kitsen wata dabbar ko fatar wasu namun daji. Bayan an gama haɗawa sai a zuba a cikin wannan kwatarniya a rufe, sai sun samu kamar mako uku, wato sun gama tsumama, sai ranar da za a fara bikin girka, za a ɗauko wannan kwatarniya a sanya ta a tsakiyar fili, a nan za a yi wa wanda za a girka wanka da wancan ruwan magani. A kuma ba shi ruwan ya sha. Haka za a riƙa yi har bayan kwanakin da sarakuanan Bori suka yanke za a gama aikin girka.

Sai kuma mawaƙin ya ci gaba da baje kolin al 'adun girka, da zayyano irin kayayyakin da ake buƙata ranar bikin girka. A nan ya ambaci za a samo 'ya'yan wuri da warki. 'Ya'yan wuri wasu fararen abubuwa ne da ake yin ɗamara da su a ka ko a ƙugu da nufin kiran iskoki ko kuma barazana ga wanda bai san dawan garin ba. Shi kuwa warki, fatar naman dawa ce ake jemewa, a tsunduma ta a cikin ruwan shuni ko Baba, da nufin ta sauya kala, sai a yi mata maɗaurai a sama da ƙasa, ana ɗaura warki a ƙugu ne, ta yadda duk wanda ya gani zai san cewa akwai wata alama ta jarumta a tattare da wanda ya ɗaura. Sai ka ga ya zauna cif a jikin mutum, hakan ya sa Hausawa ke yin Karin Magana da cewa "Warki nake dai-dai da ƙugun kowa".

A ɗango na shaɗaya kuwa sai mawaƙin ya yi yabo ga harshen Hausa Da yadda yake ganin a nan kusa yana wahala a samu wani harshe da zai iya jayayya da harshen Hausa ta fuskar al'adu. Inda yake nuna lallai harshen ba kanwar lasa ba ne, ta fuskar inganta al'adunsa. Sai kuma ya nuna irin wahalar da ake sha kafin a gama aikin girka. Har ya kwatanta aikin da Karin maganar Bahaushe da yake cewa "Hannu ɗay aba ya ɗaukar jinka". A nan yana nufin girka wani babban aiki ne, da mutum ɗaya ba zai iya yinsa ba. Dole sai an haɗa hannu da ƙarfe, kafin a kai ga nasara.

A ɗango na sha biyu, mawaƙin ya ambaci wasu ƙarin kayayyakin da bisa al'ada ake amfani da su, wajen aiwatar da aikin girka. Irin wannan kayayyaki sun haɗa da 'zobe' ko 'zobba', wato ƙawanyar da ake sa wa a hannu, su ne wanda za a girka, zai sanya su a ƙafafu da hannaye, duk da nufin idan iskokin sun iso gare shi su yarda kuma su amince su hau kan wanda ake son a girka.

13. Jagora: Sandar dargaza da 'yar bulala ɗamara tamau abin ba shakka,
    Amshi: Bauri da Bori ware bare,

14. Jagora: Kai har baƙin zane ga ƙunshi ƙafa da hannu hanyar boka,
    Amshi: Ya bankaɗo Bahaushen girka,

15. Jagora: An gabza tozali a idanu alami da goro leɓɓa toka,
    Amshi: Baubauniya rawarsu ta dauri,

16. Jagora: Da turaren wutar kiran ƙwanƙwamai Dogo da Inna na ta jiranka.

A ɗangwayen dake sama, wato na sha uku da sha huɗu da sha biyar da kuma sha shidda, Farfesan waƙa, ya ci gaba da zayyano kayayyakin da ake buƙata ne, wajen aiwatar da wannan aiki na girka. A inda ya ambaci 'Sandar dargaza da 'yar bulala, waɗannan suna daga cikin irin kayan da ake buƙata, wato ita sandar da ita ce ake wulwulawa, wato a yi ta wurga ta sama, ana cafewa, idan ana yin rawa da juyi, lokacin da ake kiran iskar da ake so ta zo. Akan yi mata kwalliya da fatoci su yi beza a jiki, kuma a yi mata ƙunshi kala-kala, yadda za ta bayar da sha'awa. Ita kuma bulalar akan rataya ta ne a jikin ɗamarar kayan da aka sa na girka. An fi amfani da wannan sanda da bulala, idan za a hau iska mai suna 'Babule', Za a ga yadda wanda za a a girka ɗin yakan sa kayan ɗamara kamar na sojoji, a tsuke ƙugu, a sanya ƙwamemen takalmi, a sa hula irin ta Soja, kamar dai Sojan gaske. Haka zai yi ta rawa yana ƙamewa, yana sara wa mutane, kuma yakan yi amfani da kalanzir yana fesa wa sama wuta na tashi, shi kuma mai garaya, ko mai goge yana ta yi masa kirari. Abin sai wanda ya gani.

A ɗango na sha huɗu kuwa, ya ɗauko salon yadda idan iskokin sun fara zuwa ne, akan samu baƙin zane gwado (na saƙi) ko kuma fari a rufe wanda za a girka a ciki. Haka zai yi ta murƙususu, duk zafin da ake yi haka zai kwanta a cikin wannan zane, ana ta gayyato masa iskoki daban-daban. Ya ci gaba da bayyana yadda Hausawa suka yarda cewa idan aka yi irin waɗannan abubuwa ne kawai iskokin za su zo. Tun farko akan yi ƙunshi, a hannu da ƙafafu, a sanya tozali a idanu ya ri raɗau. A kuma tauna goro, leɓɓa su ja wur! Duk da nufin iskokin su lamince wa wanda ake son a yi wa girka. Sai kuma a kunna wasu irin turarukan wuta, masu wani irin ƙamshi mai tayar da hankali, wanda a Bahaushiyar al'ada ake ganin da su ne ake kiran iskokin.

17. Jagora: Ɗirkaniyar kiran ‘yankogo wane mutum ya rushe girka,
    Amshi: Bauri da Bori ware bare,

18. Jagora: In an yi katarin haɗa komai sai ran shigar su wa Dokin ka,
    Amshi: Ya bankaɗo Bahaushen girka

19. Jagora: Mai kacakaura ga su Garaya sautin a gane taken Iska,
    Amshi: Baubauniya rawarsu ta dauri,

20. Jagora: Gaɗa Ira’izai an ca-cum ga Julkukuwa mutanen girka.

A ɗangwaye na 17 da 18 19 da kuma 20, Mawaƙin ya yi wani jawabi ne da nufin yana da matuƙar wahala, irin yadda tunanin Bahaushe ya ginu a kan Bori da girka, wani ko wasu da rana tsaka, su ce za su iya hana wannan addini na Bori. Kasancewar daɗaɗɗiyar al’ada ce tun kafin zuwan musulunci ƙasar Hausa. Shi yasa yake ganin ba abu ne mai sauƙi ba a iya kawo ƙarshen wannan al’ada ta Bori da girka ba a nan kusa. Sai kuma ya ci gaba da cewa, idan duk an gama harhaɗa waɗannan kayayyaki da aka ambata a baya, sai kuma a sa ranar da za a gayyato waɗannan iskoki da za su zo su hau kan wanda ake son a girka.

21. Jagora: Kafin zama Bahaushen girka kwana bakwai ake bisa girka,
    Amshi: Bauri da Bori ware bare,

22. Jagora: An sha wuyar dare da ta rana an sha tsumi na baurin girka.
    Amshi: Ya bankaɗo Bahaushen girka.

23. Jagora : Bishiya ta goruba ko tsamiya a gurin da za wanke girka,
    Amshi: Baubauniya rawarsu ta dauri,

Jagora: Wankan fita fita daga girka daɗa ya zamo Bahaushen girka

A ɗangwayen sama kuma Mawaƙin yana ƙoƙarin rufe waƙarsa da bayanin abubuwan da suke faruwa, idan an kamala aikin girka. Kamar yadda y ace ‘an sha wuyar dare da ta rana, a nan yana nufin yawan kwanakin da ake kwashewa kafin a kammmala wannan aiki kamar yadda aka yi bayani a baya. A ƙarshe kuma ya bayyana cewa bayan duk an gama irin wannan aiki na girka, shikenan mutum ya zama Bahaushen girka. wato ya zama cikakken ɗanBori, ko kuma wani ƙasurgumin boka, da ake ji da shi a yankinsu. Domin a yanzu yana da alaƙa da iskoki da yawa, da za su riƙa yi masa hidima. Suna kafa masa wasu sharuɗɗa da dokoki da zai riƙa bi. Za ka samu wani a ce kar ya sake cin nama sai kifi ko kar ya sake yin wanka, ko kuma ya yanka dabba iri kaza kamar baƙin Ɗan akuya ko baƙar Kaza, ko dai wani lamari da yake da alaƙa da bayar da magani. Su kuma waɗannan iskoki, sai yu yi ta biya masa buƙatu.

**Rataye**

| S/N | Kalma | Ma’anar Kalmar |
|---|---|---|
| 1. | Girka | Girka mutum ya zama ƊanBori |
| 2. | Baubauniya | Rawar da ‘YanBori ke yi/ faɗuwa da ake yi |
| 3. | Turjiya | Dagiya ka ƙin yin abu |
| 4. | Turka-turka | Gwagwarmayar ana tura ka kana turjewa |
| 5. | Doki | Waanda ake so Aljanu su hau kansa |
| 6. | Tsagwaro | Abu da yawa |
| 7. | Tsambauri | Tsananin bauri |
| 8. | Tsumi | Jiƙaƙƙen sassaƙe-sassaƙe da saiwoyi |
| 9. | ‘Ya’yan wuri | Hular ijiya |
| 10. | Warki | Wani bante ne na fata mai maɗaurai da ake ɗaurawa ƙugu |
| 11. | Jinka | Ɗanboto |
| 12. | Sandar dargaza | Wata sanda da ‘YnBori ke amfani da ita |
| 13. | Kacakaura | Wani abin kaɗawa mai fitar da sauti |
| 14. | Hurtumi | Ƙasurgumin namijin Sa mai tsananin faɗa |
| 15. | Asirka | Hujin hancin da ake yi wa shanun huɗa |
| 16. | Ɗirkaniya | Wani aikin da ya fi ƙarfin ka, amma k adage sai ka yi |
| 17. | Gaɗa | Wasan dandali na ‘yammata |
| 18. | Ca-cum | Taruwar abu da yawa |
| 19. | Tukku | Kaza ko Zakaran da yake da wani tudun gashi a kan sa |
| 20. | Ɓurgu | Namijin gafiya da ya gawurta |
| 21. | Ƙwanƙwabilo | Babban birnin Aljanu |
| 22. | Dogo | Sunan Aljani |
| 23. | Inna | Sunan uwar Aljanu |
| 24. | Jilkukuwa | Sunan wata Aljana |
| 25. | Ƙwanƙwamai | Jam’in sunan Aljanu |
| 26. | Iska | Sunan Aljana |
| 27. | Ira’izai | Sunan Aljanu |

# KAMMALAWA

Abin lura a wannan ‘yar muƙala shi ne, an fito da irin al’adun da ke cikin aikin bori da girka. An yi hakan ne ta amfani da waƙar ‘Bahaushen girka’ wacce ta zamo kanwa uwar gami wajen zaƙulo irin waɗannan al’adu. Haka kuma kayayyakin da ake yin girka, kamar yadda mawaƙin ya bayyana, sun taimaka ainun wajen samar da wannan takarada. Sai dai za a iya ganin sauye-sauye ko bambancin wasu al’adu a cikin wannan aiki. Ƙila hakan ya samo asali ne da yadda ƙasar Hausa ke da yawa. Kamar yadda ake samun kare-karen harshe daga waje zuwa waje, haka nan dole a samu bambancin al’adu. Kuma an kawo su ne ta yadda mawaƙin Bahaushen girka, wato Malam Sulaiman Ahmad Tijjani, mai laƙabin Farfesan waƙa ya zayyano a cikin waƙarsa.

# MANAZARTA


1. Ɗangambo, A. (1989). Rabe-raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga rayuwar Hausawa, Kano Triumph.
2. Bunza, A. M. (2009). Narambaɗa, Ibrash Islamic Publications Centre Limited Lagos.
3. Umar, M., Maijama’a, D., & Adamu, M. (2014). Conceptual exposition of the effect of inflation on bank performance. *Journal of World Economic Research*, *3*(5), 55-59.
4. Yahaya, A. B. (1997). Jigon Nazarin Waƙa. Kaduna Fisbas Media Service.
5. Uba, C. E., Heubeck, C., & Hulka, C. (2006). Evolution of the late Cenozoic Chaco foreland basin, southern Bolivia. *Basin Research*, *18*(2), 145-170.


**Cite This Article:** Yunusa Ibrahim Adamu (2021). Bori Da Girka A Bahaushen Tunani: Duba Cikin Waƙar Bahaushen Girka Ta Sulaiman A. Tijjani. *East African Scholars J Edu Humanit Lit, 4*(1), 29-34.

© East African Scholars Publisher, Kenya